# GWAJIN HALT-IT

## TAKAITACCEN BAYANI GAME DA BINCIKEN

Taranezamik asid don magance matsalar zubar jini a hanji:
Zaɓi ne na ƙasashen duniya, tare da kuma wani maganin
gwaji don samun daidaituwar gwajin

Kai (marar lafiya) kana da zubar jini a hanji da kake son a dakatar da shi da gaggawa. Dukkan magungunan da muka saba bayar wa a wannan asibiti za a cigaba da ba ka. Tare da wannan, muna gayyatar ka don ka shiga binciken. Wannan binciken zai gano ko maganin da ake kira tranexamic acid zai rage zubar jini a hanji. Muna fatan wannan bincike zai samar da kyakkyawar mafita. Mun san maganin yana taimaka wa sauran mutane masu fama da wani nau'in zubar jini amma ba a jarraba ba ko zai warkar da mai zubar jini a hanji.

A wannan bincike, rabin marasa lafiya zasu samu ainihin maganin bincike, (tranexamic acid) sannan rabin zasu samu maganin gwaji na jabu (na rage raɗaɗi). Idan ka shiga wannan bincike, kai (marar lafiya)za a ba ka maganin bincike na ainihi ko na rage raɗaɗi nan take. Za a sa maka cikin gorar ruwa tsawo sa'o'i ashirin da huɗu. Muna son mu kara karɓar bayanai game da.( na marar lafiya ) yanayin lafiyarka sai mu aika a babban ofishi a Landan.

Idan kana son ƙarin bayani game da bincikenmu yanzu, to zamu bayyana maka. Amma idan ba haka ba zamu bayyana maka nan gaba. Ko kana nufin mu cigaba da wannan bincike?

## E, ina nufin ku cigaba.

| ________________________ | _____________ | ___________________________ |
| --- | --- | --- |
| Sunan marar lafiya<br>Ko wakili | Kwanan wata | Sa hannu (dangwala hannu |

*[Ɗwannan bayani za a iya gabatar da shi ta baka Kuma ba dole sai an bi kalma da kalma ba .Zai iya dacewa da kowane irin yanayi an samar da shi a matsayin jagora ne. Ba dole ne sai an sa hannu a takarda ba idan kuma an sa hannun ba dole ne ba a ɗauka a matsayin yarjejeniya tabbatacciya ba.]*